NAZARIN JIGOGI DA SALON WASU MARUBUTA KAGAGGUN LABARAI NA KARNI NA ASHIRIN DA ƊAYA (21)

Lawal Adams
lawaladams3838@gamil.com
Da
Hauwa Muhammad Maikudi
Kano State College of Education And Preliminary Studies
hauwammaikudi@gmail.com
Da
Bashir Shehu Ibrahim
bsidanfulani@gmail.com

Tsakure

An yi wannan nazari ne a kan yadda tunanin marubuta ƙagaggun labarai a ƙarni na 21 ya canza salo yadda ya sha bamban da na ƙarni na 19 da kuma ƙarni na 20. Marubuta ƙagaggun labarai a ƙarni na 19 sun fi mayar da hankali ne wajen yin rubuce-rubuce a kan abubuwan da suka shafi addini da nasiha da jan hankali da bin dokokin ibada da sauransu. A ƙarni na 20 kuwa marubuta da yawa sun ƙaru kuma suka zo da sabon salon rubutu wanda ya bambanta da ƙarni na 19. A wannan ƙarni na 20 marubuta ƙagaggun labarai sun fi mayar da salon rubutunsu a kan abubuwan da suka shafi tarbiyya da tsafta da koya magana da mu'amala da auren dole da saka yara a makaranta, da sauransu. A wannan ƙarni aka samu jigon da ake kira "Baduniyen Jigo". A ƙarni na 21 rubuce-rubucen ƙagaggun labarai ya sake canza salo wanda ya zarta na ƙarni na 20. Wannan takarda za ta yi nazari ne kan yadda jigon ya canza salo tare da kawo misalai daga labaran litattafai da kuma labaran ake sanyawa ta gasa da kuma litattafan Adabin Kasuwar Kano. An kuma kawo wasu labaran da suka yi nasara a gasar gidauniyar Arc.Ahmed Musa Ɗangiwa 2022. An yi ƙoƙarin yin bitar ayyukan da suka gabata wanda suka haɗa da ma'anar jigo salo. An yi amfani da hanyoyin da suka haɗa da karance-karance da sauraren da ziyartar ɗakuna karatu wanda suka ba da ikon tattara bayanai. An ɗora wannan nazari kan Ra'in Mukhtar (2004). An yi ƙoƙarin kawo sakamakon nazarin da kammalawa.

Fitilun Kalmomi: Salo; Jigogi; Marubuta; Kagaggun Labarai; Karni; Ashirin Da Ɗaya

Gabatarwa

Tunanin marubuta ƙagaggun labarai a ƙarni na 21 ya canza salo ta yadda ya sha bamban da na ƙarni na 19 da kuma ƙarni na 20. Tun kafin zuwan

Addinin Musulunci ƙasar Hausa ne Hausawa suke da labarai waɗannda ake yi da ka ba a rubuce ba. Bayan zuwan addinin Muslunci ƙasar Hausa an yi rubuce-rubuce a cikin Ajami. Bayan zuwan Turawa ƙasar Hausa sai aka ci gaba da yin rubuce-rubuce da salon rubutun mutanen Romawa, wanda ake kira da rubutun boko. Marubuta ƙagaggun labarai a ƙarni na 19 sun fi mayar da hankali ne wajen yin rubuce-rubuce a kan abubuwan da suka shafi addini da nasiha da jan hankali da bin dokokin ibada da sauransu. A ƙarni na 20 kuwa marubuta da yawa sun ƙaru kuma suka zo da sabon salon rubutu wanda ya bambanta da na ƙarni na 19. A wannan ƙarni na 20 marubuta ƙagaggun labarai sun fi mayar da salon rubutunsu a kan abubuwan da suka shafi tarbiyya ko tsafta da koya magana da mu'amala da auren dole a saka yara a makaranta da sauransu. A wannan ƙarni aka samu jigon da ake kira "Baduniyen Jigo". A ƙarni na 21 rubuce-rubucen ƙagaggun labarai ya sake canza salo wanda ya zarta na ƙarni na 20.

Manufar Bincike

Manufar wannan binciken ita ce fito da nau'o'in wasu salailai waɗanda suka shafi jigogin labarai na ƙarni na ashirin da ɗaya (21) waɗanda suka haɗa da yadda salonsu yake wanda ya shafi jigo kaitsaye.

Wata manufar ita ce yadda marubutan suke amfani da jigo duniya ko fafutuka ko yadda ake sanya masu gasa domin ƙara musu ƙaimi domin su bayyana wata gudunmuwa a fagen labari

Hanyoyin Gudanar da Bincike

An yi amfani da littattafai inda aka ciro wasu maganganu da suka shafi jigo na rubutu, sannan aka mayar da su a rubuce don a nazarce su. Haka kuma, an ziyarci ɗakunan karatu nan ma an yi bitar wasu kundaye da muƙalu masu alaƙa da ƙagaggun labarai an kuma ziyarci wurin tarukan marubuta da ake gayyatar marubuta. An yi kuma amfani da na'urorin zamani domin ziyartar yanar-gizo don samun damar aiwatar da wannan binciken.

Ma'anar Salo

Masana da manazarta da dama sun yi nazari sosai, musamman a ɓangaren adabi ta hanyoyi daban-daban inda suka bayar da ma'anar salo tare da misalai kamar haka:

Ɗangambo (1981:12-13) yana ganin, salo shi ne hanyoyi ko dabarun isar da saƙo, saboda ya ƙunshi zabi cikin rubutu ko furuci kuma wani ƙari ne na daraja a cikinsu, wanda ba lalle ba ne a same shi cikin kowane rubutu ko furuci ba, wato ana iya samun lamin rubutu, maras salo. Haka kuma, ya ƙara da cewa, salo harshen wani mutum ne, wato mai bambanta na wani da wani.

Sai dai Yahya (2001:1). A fahimtarsa, yana ganin salo dabara ce ko hanyar yin kwalliya ga abu domin inganta shi ko bayyana shi. Ya bayyana cewa salo ƙwalliyar magana ce mai tasiri kan mai saurarenta. Amma Gusau (2003:54) yana kallon salo da cewa hanya ce ta nuna ƙwarewa domin nuna ƙaƙale ko wata zalaƙa wacce take ɗauke da yanga ko jan aji.

Ɗangambo (2007:38) ya ƙara bayyana salo da hanyar da ake gane dabaru ko hikimar da marubuci ya bi domin isar da saƙonsa.

Sai dai wannan nazari ya kalli salo a hanyar da marubuta ƙarni na 21 suke bi tare da dabara ko hikima ko fasaha domin su gina jigo labari da zai jawo hankalin mai karatu ko mai sauraro, ta yadda za a isar da saƙo cikin sauƙi da azanci ko hikima.

Ire-Iren Salo

A bayanan da suka gabata, an kawo bayani a kan salo tare da tsokacin manazarta adabi a kansa, ta yadda suka ba da irin ra'ayoyinsu game da salo. Ire-iren salon sun kasu gida biyar, kamar yadda Ɗangambo, (2007:38) ya bayyana su:

Miƙaƙƙen Salo : wanda shi ne na kai tsaye mai sauƙin ganewa. Wannan salo yana iya zama mai taushi ko sauƙi ta hanyar isar da saƙo ba tare da wata 'ƙawa' ko 'ado' ko 'ƙaƙale' ba. A irin wannan salo ba a faye amfani da baƙin kalmomi ba, ko wani karin harshe ko wasu kalmomi na dauri ko sababbi masu wuyar ganewa ko fahimta.

Salo Mai Armashi ko Mai Karsashi: wanda yake ɗauke da gamsarwa ta hanyar yin ƙaƙale wanda yake ɗauke da karsashi da burgewa ko ƙayatarwa.

Ragon Salo: wanda ke gundura da kashe jiki kuma ba ya da tsarin gamsarwa. Salo ne da yake tattare da sarƙarƙiya da wahalar fahimta. A wannan salo,

marubuci ko mai magana yakan yi amfani da karin harshe barkatai da kalmomin aro masu wuyar fahimta. Akan samu dawayya ko kwan-gaba kwan-baya ta yadda mai nazari ko mai saurare sai ya yi tunani mai zurfin gaske kafin ya fahimci saƙon da ke cikinshi.

Tsohon Salo da Sabon Salo: wanda kan iya kasancewa an yi amfani da tsofaffin hanyoyi ko sababbi wurin isar da saƙon. Yana iya zama gamsasshe ko akasin haka.

Salo Mai Sarƙaƙiya ko Mai Tsauri: shi ne mai wahalarwa, kuma ba a faye saurin gane shi ba saboda tsaurinsa ga saƙar manufofin ko tsauraran kalmomin da aka yi amfani da su a cikin shi. A wannan matakin na rabe-raben salo suna matuƙar taka muhimmiyar rawa wajen gano yadda marubuci ya yi ƙoƙarin rubutunsa ta yadda yake magana don ya siffanta abu ko ya bayyana ko tallata abin da yake zuciyarsa Ɗangambo (2007:38).

Kagaggun Labarai

Mukhtar (2004,shf,11) Zube yana nufin rubutun da ba waƙa ba kuma ba wasan kwaikwayo ba wato tsagoran rubutu wanda zai iya zama magana ko wata hanyar magana. Ke nan labari da akai domin bayyana wata manfa zata iya zama cikin ɓangaren zube

Asalin da Tarihin Ƙagaggun Labarai a Hausa

Mukhtar (2004,shf, 16-17) labarai sun fara suma ne bayan zuwan turawan mishan masu yaɗa addinin kiristanci a ƙasashen afrika ta yamma. A rubuce-rubucen da turawan sukai akwai J.F Schonda. Ke nan labarai ne da aka samo asalin su daga turawan yamma dake zuwa don yaɗa addini.

Rubutattun ƙagaggun labarai sun samo asali ne ɓangare biyu na farko rubutun ajami na biyu rubutun boko, inda aka baddala su zuwa rubutattun hiƙayoyi na labarai wanda aka sanya wasu cikin gasa (Yahaya1988 ,shf, 77) a lokutan da ake ba da labarai na gaske ko na almara. Tun kafin zuwan Turawan mulkin mallaka, Hausawa sun kasance suna ba da labarai waɗann da suka ƙunshi ba da labari na tatsuniya hikaya da almara tarihi da tarihihi zuwan rubutu ya sa aka mayar da wasu a rubuce wasu kuma aka baddaala su.

A shekara ta 1920, Hukumar Fassara (Translation Bureau) ta shirya wallafe-wallafen littattafan Hausa, kamar "*Alfu Laila Wa Laila*", wato *Dare Dubu Da Ɗaya*, wanda ya ƙunshi hiƙayoyi Larabawa. Daga baya, a 1933, Daraktan

Ilmi na Jihar Arewa, Hanns Vischer (Ɗan Hausa), ya ƙaddamar da gasa ta rubuta ƙagaggun labarai don ƙara haɓaka rubutun zube na Hausa.

Malumfashi (2019,shf ,76,77) ƙugiyar CMS ta taka muhimmiyar rawa wajen samar da wani rukun a cikin adabin Hausa inda ta raba su daban-daban zuwa mai suna ***Littafi Na Karantawa Da Fari*** a shekarar 1932. Bayan wannan ta samar da littafi mai suna ***Fatima*** *a 1933*. Baya da wannan an samu wasu litattafan na rubutun zube na Hausa.

A ƙarni na 21, ƙagaggun labarai a cikin adabin Hausa sun ci gaba da bunƙasa, saboda tasirin al'adu da fasaha, da gasanni irin su "*Hikayata ta BBC Hausa*" da a gasar gidauniyar Arc.Ahmed Musa Ɗangiwa duk waɗan nan suna ƙara fito da iririn jigogin kuma irin labarai sun kasu kashi daban-daban dangane da salo da kuma maƙasudan yin su. Airin waɗanan maƙasudansun haɗa da yadda ƙarnin yake tafiya tare da tunanin mutane

Ire-iren Jigogin Ƙagaggun Labarai A Karni Na 21

- Nasiha
- Soyayya
- Zamantakewa
- Siyasa
- Fafutuka ('Yancin mata) da sauran su

Ire-iren Ƙagaggun Labarai da Suka Fi Shahara A Karni Na 21

Waɗannan labarai suna mai da hankali ne a kan rayuwar yau da kullum da matsalolin al'umma da al'adun Hausa. Suna nuna yadda mutane suke fuskantar ƙalubale kamar talaucida rashin adalci, ko sauye-sauyen zamani.

Sara suka na Fatima Bello (a gasar gidauniyar Arc.Ahmed Musa Ɗangiwa, 2022 littafin Ɗaukar Jinka) yana nuna matsalolin da ke cikin al'umma, kamar rashin jituwa ko tasirin zamani.

Salo: Yawanci marubutan suna amfani da harshe mai sauƙin fahimta da kuma misalai na yau da kullum don sa ma mai karatu ya ji kamar yana cikin labarin da suke bayarwa.

Muhimmanci: Suna taimakawa wajen fahimtar matsalolin zamantakewa kamar auren dole, shaye-shaye, ko rashin ilimi.

Kagaggun Labarai na Soyayya

Waɗannan labarai sun fi shahara a tsakanin matasa, kuma suna magana game da soyayya ko alaƙa da rikice-rikice masu nasaba da ita. A ƙarni na 21, sun ƙara nuna tasirin fasaha kamar wayar salula da shafukan sada zumunta.

Misali: A gasar Hikayata, labarai kamar *Gudun Gara* na Amira Souley sun nuna yadda soyayya ke tasowa a cikin al'adun Hausawa na zamani, kamar ta hanyar WhatsApp ko Instagram.

Salo. Suna da ban dariya, ban tausayi, ko kuma juyi a ƙarshe wanda ke sa mai karatu ya ji daɗi.

Muhimmanci: Suna ƙarfafa matasa su rubuta labarai masu alaƙa da rayuwarsu, kuma suna taimakawa wajen nuna sauye-sauyen al'adun soyayya.

Kagaggun Labarai na Ilimi da Koyo

Waɗannan labarai suna da maƙasudin koyar da darasi ko ilimantarwa game da muhimman abubuwa kamar lafiya da ilimi ko ƙa'idodin rayuwa. A ƙarni na 21, suna magana game da batutuwa kamar HIƁ/AIDS ko sauyin yanayi, ko tasirin fasaha.

Misali. Wasu labarai a gasar Hikayata sun taɓa batun yadda yara suke fama da rashin ilimi ko kuma yadda cututtuka ke shafar al'umma.

Salo: Yawanci suna da harshe mai sauƙi da kuma darasi a ƙarshe wanda ke sa mai karatu ya ji an ƙarfafa shi.

Muhimmanci: Marubutan suna taimakawa wajen wayar da kan jama'a game da batutuwa masu muhimmanci a cikin al'umma kamar neman ilmi da haƙuri riƙon amana da tsafta da sana'a da sauransu.

Nazarin Wasu Littatafai na Karni na Ashirin da Ɗaya (21)

Kamar yadda binciken ya bayyana a sama, ya kawo wasu daga cikin jigogin ƙagaggun labarai na ƙarni na 21. A nan za a yi nazarin wasu daga cikin littattafan ƙarnin ne domin a bayyana yadda aka samu sauyawar salon rubutun ƙagaggun labarai daga salon ƙarni na 20 zuwa salon ƙarni na 21. Hakan ya biyo bayan halin da marubutan suke ciki, domin shi salo yana tafiya ne da zamani da kuma halin da zamanin yake ciki. Wato in kiɗa ya canza, rawa ma sai ta canza. Bayan ƙoƙarin da marubuta ƙarni na 19 da na 20 suka yi, sai ya kasance al'ummar Hausawa sun sami kansu a cikin rayuwa ta daban wanda hakan ya janyo su ma marubuta a wannan ƙarni suka canza salo zuwa kan abubuwan da mutane suka fi buƙata. Ga wasu daga cikin ire-iren jigon da littattafan ƙarnin na 21 suka ƙunsa.

Fafutuka: Marubuta da yawa sun yi rubuce-rubuce a kan fafutukar neman ‘yancin mata, don ganin su wayar wa da mata kai a kan abun da suka kira “Bauta ko take haƙƙi”. Daga cikin ire-iren wannan salo akwai:

Littafi: Wa Zai Auri Jahila

Wannan littafi ya bayyana ire-iren fadi tashi da gwagwarmayar da mata suke sha a rayuwa da ire-iren tsangwama da tauye haƙƙin da ake yi musu tun daga haihuwa har zuwa aure da neman ilmi. Marubucin ba iya haka ta tsaya ba har sai da ya nuna yadda wasu suke lalata mata tare ƙuntata masu. Akwai inda marubucin yake cewa:

> *“Ilimi shi ne hasken da ke fitar da mace daga duhun raini da bautar da al’umma ta jima tana yi mata”……*(*Ado Ahmad Gidan Dabino:* shf. 21)

Wannan batun yana wakiltar fafutukar mata wajen neman ilimi, da kuma ƙin yarda da tsarin da ke tauye musu haƙƙinsu. Littafin ya mayar da hankali kan wayar da kai game da muhimmancin ilimin ’ya’ya mata a cikin al’ummar Hausawa da mutane arewa.

Zamantakewa: Shi ma wannan salo ne da marubuta da yawa suke rubucr-rubuce a kansa. A mafi yawa na ire-iren wannan salo ko jigo ana samun yadda marubutan ke nuna dadin zama ga ma’aurata da ‘yanuwa da dangi ko kuma akasin haka a cikin rubece-rubucensu. Daga cikinsu akwai;

Littafi: *Daukar jinka*

Marubuciyar ta yi ƙoƙarin nuna yadda halaye na tsakanin namiji da mace ke wakana da zaman haƙuri musamman mata yadda suke fuskantar ƙalubale. A labarin marubuciyar ta nuna yadda take shan wahala a gidan aure da kuma yadda ta riƙe ta aman da haƙuri,. Mu duba wannan matanin daga cikin littafin:

> *“……..Tun a farkon aurenmu na fara fuskantar matsala, duka da rashin yadda, ban isa in yi huldda da mutane ba. Haka haƙura na zauna tunda yana daukar dawainiyata kuma ba ni da matsalar kudi har ina taimakawa ‘yan’uwana, a haka har muka haifi*

'ya'yanmu uku da shi maza biyu mace ɗaya itace ƙarama……..”(Maraici ko son zuciya?: sh. 105)

Lallai wannan labarin ya bayyana yadda wata mata take haƙuri a zamantakewar zaman aure wanda yake ɗauke da ƙalubale musamman yadda take shan wahala na rashin yarda da kuma dukanta da yake yi. Wannan yake bayyana cewa akwai masu irin wannan rayuwar a cikin wannan zamanin

Faɗakarwa: Na ɗaya daga cikin jigogin da marubuta ƙarni na 21 da ɗaya suka mayar da salon rubuce-rubucensu a kansu. Faɗakarwa na karkata ne a kan yadda ake nuna wasu ɗabi'u da halaye waɗanda ba su da kyau ga jama'a.

Littafi: *Ummalkhairi*

A littafin marubucin ya nuna yadda wasu ɗalibai suke rayuwar shiririta ta lalacewa a lokacin da suka je jami'a. Ya nuna iren-iren ƙalubalen da waɗannan ɗalibai suke fuskanta a rayuwarsu da kuma yadda karshensu yake kasancewa. Ga matanin kamar haka:

“Na ji daɗin jami'a, na kece raini na burge na kuma sheƙe ayata yadda nake so, amma bayan lokaci ya ƙure mani na gane cewa tsawon lokaci da na ɗauka ina saɓon Allah, lokaci ne wanda na yi asarar sa na cuci kaina. Duk ta ƙare ga inda na samu kaina. Wallahi gaskiyar Jamila da take cewa “kyakkyawan ƙarshe yana ga masu tsoron Allah”……..”(*Ummalkhairi: sh.65*).

Wannan labarin ya yi faɗakarwa ne ga wasu mutane masu irin rayuwar alfahari da ɗaukar duniaya da faɗi inda daga ƙarshe rayuwar ta koma ta ƙasƙanci da kuma nadama kamar yadda wannan matar take faɗa. Labarin yana ɗauke da ƙalubale wan ake son mutum ya koyi wani darasi musamman yadda ya faɗakar tin farkon samun dama kafin ta kufce.

Nasiha: ta ɗaya daga cikin jigogin da marubuta ƙarni na 21 da ɗaya suka mayar da salon rubuce- rubucensu a kansu. Nasiha na jingina ne a kan yadda ake nuna wasu ɗabi'u da halaye waɗanda ba su da kyau ga jama'a da kuma yadda za a maganace wata matsala.

Littafi: *Ɗaukar Jinka*

A labarin marubucin ya nuna yadda wasu ɗalibai suke rayuwar shiririta ta lalacewa a lokacin da suka je jami'a. Ya nuna iren-iren ƙalubalen da waɗannan matasa suke fuskanta a rayuwarsu da kuma yadda ƙarshensu yake kasancewa. Ga abin da aka tsakuro daga littafin kamar haka:

> *"na ya da tsarin gidan gyaran hali sosai, tabbas sunan nasa ya dace da shi, musamman bisa tasirinsa na sauya mummunar ɗabi'a zuwa kyakkyawa"……."(Sara Suka: sh. 49)*

Labarin ya yi nasiha ne musamman wanda suke shaye-shaye da safarar kayan maye. Labarin yana nasiha ne ga matasa masu irin rayuwa wacce take barazana ga al'umma kuma an fito da yadda gidan gyaran hali yake wanke tunaninsu da taimakon su zu ga rayuwa mai kyau

Soyayya: Ita ce yarda dabin da ake so a zuciya domin samun natsuwa ko hanyar da mutum yake yin wasu dabaru don samun farin ciki, a rayuwar yau da kullum, ko zata iya zama neman abu don a same shi wanda zata iya gushewa da zarar an samu abin da ake so ko ta ƙara bijirowa ta wata sigar wacce ba a kanta aka gina rayuwar baya ba. Ita ma tana ɗaya daga cikin jigogin da marubuta ƙarni na 21 da ɗaya suka mayar da salon rubuce-rubucensu a kansu musamman matasa. Soyayya na inganta ne a kan yadda ake nuna wasu ɗabi'u da halaye tsakanin taurari maza da mata musamman matasa.

Littafi: *Goran Duma*

A labarin marubuciyar ta nuna yadda wasu taurari suke rayuwar soyayya a lokacin da suke kan ganiyar samartaka. Ya nuna iren-iren ƙalubalen da waɗannan matasa suka fuskanta a rayuwarsu kan soyayya.

> *"haka ne, motar haya na hawo. Ya ɗan yi dariyar da yake tunanin za ta sami matsuguni a zuciyarta. Ya ce….."(Goran Duma: sh.46)*

A cikin labarin marubuciyar ta yi ƙoƙarin bayyana wasu taurari yadda suke rayuwar soyayya a lokacin da suke kan ganiyar samartaka. Wannan ya

bayyana jigon soyayya waɗannan matasa suke yi a rayuwarsu cikin wannan ƙarnin na ashirin da ɗaya.

Siyasa: Lallai jigon siyasa yana ya ɗaya daga cikin jigogin da marubuta ƙarni na 21 da ɗaya suka mayar da salon rubuce-rubucensu a kansu. Siyasa na jingina ne a kan yadda ake nuna wasu ɗabi'u da halaye waɗanda ba su da kyau ga jama'a da kuma yadda za a maganace wata matsalolin rayuwa.

Littafi: Dimokuraɗiyya

A labarin marubucin ya nuna yadda wasu yadda masu mulki ke yin yadda suka ga dama ba tare da duba raywar mutanen baya ba. Ya bayyana iren-iren ƙalubalen da ke sanya matasa rashin neman ilmi da kuma yadda suke fuskantar rashin tabbas a rayuwarsu da karshensu yake kasancewa kan bin 'iyan siyasa da maƙalema uban gida.

"Dimokuraɗiyya ta zama suna kawai; aiki kuwa na hannun 'yan tsiraru." ……..*"(*Kabiru Gwangwazo shf 21*)*

A cikin wannan batun an nuna yadda marubucin ya fallasa dambarwar siyasa, inda shugabanci ke tafiya bisa son rai da kariyar masu laifi, abin da ake kira siyasar uban gida ko ta 'yan'uwa da abokai da kuma yadda masu mulkin kesamun kariya ga manyansu.

Kammalawa

Wannan nazarin ya yi ƙoƙarin bayyana wasu muhimman salo da jigogi na ƙarnin 21 tare da kawo misalai daga wasu labarai da aka sanya su cikin gasa da kuma wasu litattafai inda aka bayar da misalan tare da kawo lambobin shafikan da batun ya faru.

A wannan ƙarni na ashirin da ɗaya (21) marubuta ƙagaggun labarai sun fi mayar da salon rubutunsu a kan abubuwan da suka shafi tarbiyya ko tsafta, koya Magana, mu'amala, auren dole, saka yara makaranta, da sauran su. A wannan ƙarni aka samu jigon da ake kira "Baduniyen Jigo". A ƙarni na 21 rubuce-rubucen ƙagaggun labarai ya sake canza salo wanda ya zarta na ƙarni na 20 da na 19 inda aka samu jigogi da kuma kafafen sadarwar zamani.

Manazarta

Adams, L. (2025). "Nazarin Salon Labartawa A Wasu Waƙoƙin Baka Na Hausa". Kundin Digiri na Biyu, Jami'ar Umaru Musa Yar'adua, Katsina

Abdulrahman, A. J. Y (2022). Ɗaukar Jinka Labaran Da Suka Samu Nasara A Gasar Arc. Ahmaed Musa Ɗangiwa 2022; Ɗangiwa Literary Foundation.

Bbc Hausa gasar Hikayata 2022 da 2023 da 2024/facebook.com Bbchausa.com

Bal, M. (1985). *The Theorie Ban Bertellen en Berhalen*. Muiderberg: Coutinho.

Ɗangambo, A. (2007). *Ɗaurayar Gadon Feɗe Waƙa.* Amana Published.

Ɗangambo, A (1981). 'Daurayar Gadon Feɗe Waƙa', Takardar da Aka Gabatar a Taron Kara wa Juna Sani: Ƙungiyar Harshen Hausa,Kwalejin Ilmi.

Gidan Dabino, A. A. (2004). Wa Zai Auri Jahila? Ibadan: Spectrum Books Ltd,

Gusau, S. M. (2003*). Jagoran Nazarin Waƙar Baka*, Benchmark Publishers Limited.

Gusau S. M. (2008). *Dabarun Nazarin Adabin Hausa,* Benchmark Publishers Limited,

Genette, G. (1972). *Narratiɓe Discourse*. Trans. Jane E. Lewin Ithaka: Cornell. Blackwell Basil. Oɗford Uniɓersity Press.

Gwangwazo, K. (2011). Dimokuraɗiyya. Kano: Kano State Publishers.

Maimunatu, I. S. B (2014) *Goran Duma 1.* Iyaruwa Publishers, Kano.

Malumfashi, I. A. Ed. (2019). *Labarin Hausa A Rubuce* (1927-2018). A Festschrift in Honour of Dalhatu Muhammad. Department of African Languages and cultures, Zaria Ahmadu Bello Uniɓersity.

Mukhtar, I. (2004). *Introduction To Stylistic Theorics Practice And Criticisms*. Country Side Publishers.

Rasheed, U. A. (2017). "Nazarin Salon Labartawa daga Wasu Wa'azozin Sheikh Kabir Haruna Gombe". Kundin Digiri na Ɗaya, Jami'ar Umaru Musa Yar'adua Katsina.

Yahya, A. B.(2001). *Salo Asirin Waƙa*, Fisbas Media Serɓices